# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Farkon fara samun damuwan Mutum




Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Byron Unger; Lazarus
Alastair Paterson

Fassarawa: Maren Dameng Daniel

Mai niyyan daukan nauyi: M. Maillot; Tammy S.


Labari na daya 2 daga cikin sittin 60


**www.M1914.org**

***Bible for Children,*** *PO Box 3, Winnipeg, MB R3C 2G1 Canada*



Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.


Hausa








Bayan da Hauwa'u tayi rashin ɗa'a ta karya dokan Allah tayi zunubi sai ta rinjayi Adamu ma yaci 'ya'yan itacen.

3



A lokocin da Adamu da Hauwa'u sunka yi zunubi, dukkansu sun san da cewa suna tsirara. Sai su ka nemi ganye suka ɗinka bante, su ka kuma ɓuya a cikin daji daga wurin Allah.

4



A cikin sanyin yammaci Allah ya zo cikin lambu. Ya kuma san abin da Adamu da Hauwa'u suka yi. Adamu ya daura laifin wa Hauwa'u. Hauwa'u kuma ta daura laifin wa maciji. Sai Allah ya tsine ma macijin, matar kuma za ta ji zafi wurin haihuwa. Adamu domin kayi zunubi, an la'anci kasa da ƙaya da sarƙaƙƙiya sai kasha wahala kafin ka sami abinci.

5



Sai ubangiji Allah ya kore Adamu da Hauwa'u daga cikin Lambu. Domin sunyi zunubi, an raba su da Allah mai bu sa rai. Allah ya kuwa sa adda mai wuta ya kore su. Ya kuma mawa Adamu da Hauwa'u rigan sawan fata. Ina ne ubangiji Allah ya samo wanan fatan?

6



A cikin lokaci, lyalai sun fito daga cikin Adamu da Hauwa'u. Ɗan su na farko, kahilu shi manomi ne. Ɗan su nabiyui habila shi ma kiyayi ne. Wata tana ƙabilu ya kawo kyautar abunda ya girba wa Allah. Habila kuma ya zabo mai kyau da ga cikin dabobin sa, ya ma Allah kyautar hadaya. Allah kuwa ya ji daɗin kyautar Habila.

7



Allah kuwa bai ji daɗin kyautar ƙabila ba sai ƙabila kuwu ya ji haushi. Sai Allah ya ce, “Idan ka yi abu mai kyau, Bazan karɓa bane?”

8


Fushin ƙabila bai ƙareba.  Wata rana a fili ya kashe Habila.
9


Allah ya kuwa yi magana da ƙabila.  “Ina ɗan'uwanka Habila?”  “Ban sani ba,” ƙabila ya yi ƙarya.  “Ni ke ajiyar ɗan'uwa na?”  Sai Allah ya horashi ta wurin karbar basiran sa na noma, ya sa shi ya zama mai yawo barkate.
10


Ƙabila ya fita da ga gaɓar ubangiji.  Ya yi aure ya auri 'yar gidan Adamu da Hauwa'u.  Su ma sun samu lyali. Ba'a jima ba, jikokin ƙabilu da kum tattaba kunne sun cika garin da ya kafa.
11


Iyalen Adamu da Hauwa'u sun cika kuwa.  A wancan lokacin mutane su na tsawon rai ba kamar yanzu ba.
12


Lokacin da ta haifi ɗanta Seti, Hauwa'u tace, “Allah ya bani Seti domin ya maye gurbin Habila.” Seti kuwa mutumin Allah ne, ya yi rayuwa har na tsawon shekaru 912 kuma ya haifi yara da yawa.
13


A cikin duniya, mutane sun zama masu mugunta daga wannan zuriyyan zuwa wani zuriyan. A ƙarshe Allah ya ce ya hallaka dukan mutune.  Dukkan dabobi da tsuntsaye. Allah yayi dana sanin halittan mutum.  Amma mutum daya ya gamshi Allah ...
14

Wanan mutumin sunan sa Nuhu. Ɗan gidan Seti, Nuhu kuwa mutumin kirki ne. Ya yi tafiya da Allah. Ya kuma koyawa yaran sa, maza uku yanda za su biyyya ga Allah. Yanzu Allah ya shirya amfani da Nuhu ta waje na musamman.



15

Farkon fara samun damuwan Mutum

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Farawa 3-6

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

Allah ya san da cewa munyi abubuwan da basu da kyau, wanda a ƙira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne.

Allah yana kaunan mu sosai Ya kuma aiko da ɗansa, Yesu, domin ya mutu a kan giciye, kuma ya biya sakamakon zunuban mu. Yesu ya tashi kuma ya koma sama! Yanzu Allah zai yafe mana zunuban mu.

Idan kana so ka juyo daga zunuban ka, ka faɗawa Allah wannan: Ya Allah, na bada gaskiya ga Yesu ya mutu domina kuma yanzu ya na yare. Ina rokon ka, ka shigo cikin zuciyana kuma ka yafe min zunubai na domin na samu sabon rai kuma na zauna da kai har abada. Ka taimakeni in yi rayuwa da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amen. Yahaya 3:16

Ka karanta littafi mai-tsarki ka kuma yi Magana da Allah a kulla yamin!